# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tudun mun tsira – Mai bayani a kan ’yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai
## Kashi na biyu: Dabara ta rage ga mai shiga rijiya


Wadda ta rubuta: Chrispin Mwakideu

Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja

Wadda ta tace: Halima C. Schmaling


**’Yan Wasa:**

Lami: ’yar shekara 20

Ma’aikacin ofishin jakadanci: ɗan shekara 45

Faisal: ɗan shekara 19

Suleman: ɗan shekara 19

Malam Talle: ɗan shekara 60

Matar M. Talle: ’yar shekara 55

Magaji: ɗan shekara 22

**Mai gabatarwa:**

Jama'a, barkanmu da sake saduwa a shirinmu na "Ji Ka Karu". Wannan shi ne kashi na biyu a wasan kwaikwayonmu, mai taken "Tudun Mun Tsira – Mai bayani a kan 'yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai". A kashi na farko, mun fahimci yadda rayuwar wasu matasa ta sa gaba: akwai Faisal, ɗan Arewacin Afirka wanda yake sha'awar yin ƙaura zuwa Turai tare da abokinsa Suleman. Ga kuma Magaji wanda shi ma ɗan wata ƙasar Afirka ne da bai daɗe da kammala karatunsa na jami'a ba, sai kuma Lami wadda budurwar Magaji ce da ta tsinci kanta a tsaka mai wuya. Sannan kuma mun san iyayen Lami waɗanda suke ta faɗi-tashi don ganin sun tura 'yarsu zuwa Turai don ta yi karatun lauya. To ko yaya za ta kaya? Ku biyo mu don ku ji yadda wannan wasan namu mai suna "Dabara ta rage ga mai shiga rijiya" zai kasance. Bari mu fara da sauraron yadda wani jami'in ofishin jakadanci ke yi wa Lami tambayoyi don ba ta bizar tafiya karatu.

**Fitowa ta 1: Ana ganawa da Lami don samun bizar tafiya karatu**

**Ma'aikacin ofishin jakadanci:** Ina Lami Talle! … Ina Lami Talle take ne?

**Lami:** Ni ake kira? Yi haƙuri, ga ni nan Yallaɓai.

**Ma'aikacin o. j.:** Ke yarinya, nan fa ba hotal ba ne. Taso!

**Lami:** Don Allah ka yi haƙuri, Yallaɓai.

**Ma'aikacin o. j.:** Ba ki da lafiya ne Lami?

**Lami:** Kalau nake Yallaɓai, tsabar bin layi ne wanda sai da ya sa na kwana a waje. Ban ma sami yin barci sosai ba.

**Ma'aikacin o. j.:** Mutane masu neman biza sai ƙaruwa suke duk shekara. Kin san wannan ba ƙaramin aiki ba ne gare mu. To, me ya

sa kike son zuwa Turai?

**Lami:** A, don na... don na yi karatu.

**Ma'aikacin o. j.:** Mhm... karatu ko? To me za ki karanta?

**Lami:** Zan yi karatun lauya ne. Akwai dukkanin bayanan a cikin…

**Ma'aikacin o. j.:** Na san abin da ke cikin fayil ɗinki. Ina so ki ba ni amsa kai tsaye. Ba wata jami'a a nan ko a wata ƙasar Afirka da ake yin irin wannan karatun? Ina ganin wannan zai fi miki sauƙi.

**Lami:** Gaskiya akwai, sai dai ba su yi suna kamar waɗanda suke a Turai ba. Zan fi samun aiki mai tsoka in dai na yi digirina a Turai.

**Ma'aikacin o. j.:** Wa zai biya kuɗin ɗawainiyar karatun naki?

**Lami:** Iyayena mana. Sun ma riga sun biya kuɗin karatun zango na farko. Ta ɓangaren wurin zama kuma, a *hostel* ɗin ɗalibai na jami'ar zan zauna.

**Ma'aikacin o. j.:** Karatun naki fa na shekara uku ne. Wa zai biya sauran?

**Lami:** E to, ina zato iyayen nawa ne, tun da su suka tura ni karatu waje.

**Ma'aikacin o. j.:** Kina zato? Wannan ba maganar zato ba ce. Ina son na san takamaimai wa zai ɗauki nauyin karatunki a Turai ? Mece ce sana'ar iyayen naki?

**Lami:** Ma'aikatan gwamnati ne.

**Ma'aikacin o. j.:** Kin san nawa suke ɗauka dukansu biyun a wata?

**Lami:** Umm… ba na ce ba Yallaɓai. Amma takardun bayanin albashin nasu…

**Ma'aikacin o. j.:** Na gaya miki, na karanta fayil ɗinki duka. Ki ba ni amsar tambayar da na yi miki kawai. Wato ba ki san nawa albashin nasu yake ba ko?

**Lami:** Yallaɓai, ka yi min uzuri. Ba na sa ido a kan ko nawa iyayena suke ɗauka. Ni kuma ban taɓa tambayarsu ba, haka su ma ba su taɓa faɗa mini ba.

**Ma'aikacin o. j.:** Kina da niyyar dawowa kasarku in kin kammala karatun naki?

**Lami:** Ina da niyyar hakan.

**Ma'aikacin o. j.:** Ta yaya zan iya tabbatar da hakan? Ta yaya zan tabbatar da cewa idan na ba ki biza za ki dawo a kan lokaci?

**Lami:** Saboda ina da wanda zan aura a nan.

**Ma'aikacin o. j.:** Haka ne? Kai madalla, ina taya ki murna! Yaushe za a yi bikin Malama Lami?

**Lami:** Sai na… kammala karatuna… Yallaɓai.

**Ma'aikacin o. j.:** Ba laifi! Shi ke nan.

**Lami:** Shi ke nan?

**Ma'aikacin o. j.:** Zan ba ki biza, Malama Lami, amma sai kin biya kuɗin da ake biya na ƙa'ida, wato Yuro 60. Ki je ki biya a wurin kashiya, za ta ba ki rasit. Ina taya ki murnar samun mijin da kika yi, Allah Ya ba da sa'ar karatu.

**Lami:** Na gode Yallaɓai! Na gode ƙwarai da gaske! Allah Ya saka da alheri! Na gode.

**Ma'aikacin o. j.:** To madalla.

**Mai ba da labari:**

Duk wanda ya taɓa neman bizar zuwa Turai ya san ba abu ne mai sauƙi ba. Duk da cewa ana hana mutane da dama bizar, wannan ba ya hana su gwada sa'arsu. Lami na ɗaya daga cikin waɗanda suka yi sa'a. A daidai lokacin da Lami ta fito daga ofishin jakadancin cike da farin ciki da ɗoki, a can arewacin Afirka kuma, ga Faisal can ya haɗu da abokinsa Suleman. Ga irin hirar da suke yi.

**Fitowa ta 2: Faisal da Suleman a gaɓar teku**

**Suleman:** Kai! Haba Faisal! Kanka ɗaya kuwa!

**Faisal:** Ka ga Suleman, wannan ita kaɗai ce mafita. Za ka biyo ni ko kuwa?

**Suleman:** Ina so na bi ka, amma ina jin tsoro. Yanzu kai ba ka jin tsoro, Faisal?

**Faisal:** Tsoro fa ka ce? Na me? Ba mamaki fa mu yi nasara, amma idan ba mu gwada ba, ai ka ga ta yiwu mu yi asara!

**Suleman:** Kana ganin abin zai yiwu kuwa?

**Faisal:** A'a, ba ni da tabbas Suleman. Amma ya kamata mu gwada. Idan kuma aka kama mu, to fa komai ya wargaje ke nan.

**Suleman:** To, mu sake wata hanya mai dama-dama mana. Gaskiya wannan tunanin naka yana da haɗari sosai, Faisal.

**Faisal:** Sauran hanyoyin kowa ya san su. Kwanakin baya ma an kama wasu 'yan gudun hijira a wani kwale-kwale dab da gaɓar tekun Turai. Ka san me ya same su?

**Suleman:** Harbe su aka yi ko?

**Faisal:** A'a, ba harbe su aka yi ba. Ai ba za a kashe su haka nan ziƙau ba! 'Yan gudun hijira ai ba masu laifi ba ne. Kamo su dai kawai aka yi.

**Suleman:** Af to… Ai yanzu na gane. Wato za ka kauce wa na'urar gano mutane ke nan, shi ya sa ka ce wannan sabuwar dabara ce. To, babu laifi. Amma kana ganin za mu faɗa wa iyalanmu da 'yan'uwanmu kuwa?

**Faisal:** Za mu faɗa musu mana, amma dai sai mun isa Turai tukuna.

**Suleman:** To kuma in ba mu yi nasarar isa can ɗin ba fa?

**Faisal:** Sai mu yi ta gwada sa'armu.

**Mai ba da labari:**

Da alama Faisal ya samo wata dabarar kutsawa Turai ta haramtacciyar hanya.

Ko yaya wannan dabara take? Shin zai yi nasara kuwa? Shin Suleman zai bi shi kuwa? Ko zai canza shawara? Haka dai wannan gwagwarmayar ta ci gaba. Can kuma, Lami ta karɓi takardar bizarta. Ga ta can ma a gida tana nuna wa iyayenta.

**Fitowa ta 3: A gidan su Lami**

**Matar M. Talle:** Kai, amma Lami, yau kin nuna min cewa kin haifu. Ina alfahari da ke wallahi!

**Malam Talle:** Ai, ni ma tunanina ke nan. Ba ni in sake ganin bizar nan.

**Lami:** Haba Baba, har sau nawa za ka gani? To shi ke nan, ga ta.

**Malam Talle:** Lami Talle, takardar bizar karatu a Turai ta tsawon shekaru uku. Za a iya amfani da ita sau da yawa. Me kuma sau da yawa yake nufi? Ko ana nufin mu ma za mu iya amfani da bizar taki mu je Turai?

**Lami:** A'a Baba, ana nufin zan iya shiga Turai ko sau nawa ne matuƙar bizar tana aiki.

**Malam Talle:** To, na gane. Ai shi ke nan. Lami, na riga na tanadar miki da tikitin jirgi. A ƙarshen wannan satin ma za ki tashi.

**Lami:** Karshen wannan satin? Haba Baba, ai ban shirya ba! Ban yi sayayya ba, ban haɗa 'yan kayayyakina ba, ban kuma yi sallama da…

**Malam Talle:** Kada ki ga laifina. Babarki ce ta tsara hakan.

**Matar M. Talle:** Kin ga 'yata, ya kamata ki hanzarta ki bar ƙasar nan. Ina

tsoron kada a soke wannan bizar taki. Yadda kika faɗa mana yanayinsu, kin san komai na iya faruwa.

**Lami:** Bari in je waje na amsa wayar nan.

**Matar M. Talle:** To Lami, je ki ki amsa. Ki gaishe da Magaji, ki faɗa masa ya kamata ya zo, ya daɗe bai leƙo ba.

**Lami:** Hello Magaji, yaya kake?

**Magaji (ta waya):** Gaskiya kike so na faɗa miki ko kuma rufa-rufa?

**Lami:** Ka san na fi son na ji gaskiya. Don Allah ka yi haƙuri, ran nan na baro ka ba sallama. Amma…

**Magaji:** Share kawai Lami. Yaya kin sami bizar? Akwai wani abokina da ya nemi biza zuwa Turai kwanan nan bai samu ba. Na ji cewa yanzu sun matsa.

**Lami:** Haka ne, amma ni na samu, Magaji. Kuma yanzun nan Baba yake faɗa mini cewa ƙarshen satin nan zan tashi zuwa Turai.

**Magaji:** Me kike cewa? Don Allah ki daina tsokanata. Karshen satin ai ya taho.

**Lami:** Na sani Magaji. Don Allah ka yi haƙuri, nan ba da daɗewa ba za mu yi bankwana.

**Magaji:** Ba komai Lami. Ni dai ina taya ki murna kuma ina alfahari da ke sosai.

**Lami:** Na gode Magaji. Na ji daɗin jin hakan daga bakinka.

**Magaji:** Wato dai yanzu za mu yi sallama da juna ke nan, ta waya?

**Lami:** Anya kuwa? Mama ta ce ka zo. Zan kuma so mu gana kafin na tafi. Akwai abin da nake so na faɗa maka.

**Magaji:** Abin mai daɗin ji ne kuwa?

**Lami:** Mhmm… ina jin mai daɗin ji ne.

**Magaji:** To, alhamdu lillahi. Shi ke nan, ki faɗa mata na ji daɗin wannan gayyatar. Zan zo gobe da daddare in hakan ya yi.

**Lami:** Ya yi. Sai goben ke nan.

**Mai gabatarwa:**
Karshen wayar Lami da Magaji ya zo daidai da ƙarshen wannan wasan na yau, mai suna "Tudun mun tsira – Mai bayani a kan ƙaurar 'yan Afirka zuwa Turai". Yanzu dai Lami ta sami biza kuma an yi mata tanadin tafiya zuwa Turai. To ko me za ta tarar a can? Yaya Magaji zai ji idan ta tafi? A can kuma gaɓar tekun arewacin Afirka, shin su Faisal da Suleman za su aiwatar da shirinsu na kutsawa Turai ta ɓarauniyar hanya? Za ku ji yadda za ta kaya a cikin kashi na uku.
Ku biyo mu a shafinmu na facebook.com/dw.Ibe don tattaunawa, ku kuma faɗi ra'ayinku a kan hanyoyin gudun hijira da suka dace, da kuma haramtattun hanyoyin. Ku huta lafiya.